Babu wani mutum da zai yi mini sallama har sai Allah Ya dawo mini da raina har sai na mayar masa da sallamar

Daga Abu Huraira Allah - Ya yarda da shi - cewa Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata a gare shi ya ce: "Babu wani mutum da zai yi mini sallama har sai Allah Ya dawo mini da raina har sai na mayar masa da sallamar".

[Sanadinsa Hasan ne] [Abu Dawud ne ya Rawaito shi da Kuma Ahmad]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana bada labarin cewa shi ana dawo masa da ransa dan ya amsa sallama ga dukkan wanda ya yi masa sallama , daidai ne ya kasance a kusa yake ko a nesa; rayuwar barzahu da ƙabarbura wani al'amari ne na gaibu, babu wanda ya san haƙiƙaninsu sai Allah, Shi Mai iko ne akan dukkan komai.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/6222